# *Waye ne Yesu?*

*‘Ba wa’azin kanmu muke yi ba, sai dai na Yesu Kristi, a kan shi ne Ubangiji, mu kuma bayinku saboda Yesu...’*

2 Korintiyawa 4:5

*Peter Walker*
**www.1peter1three.weebly.com**

*Wanan litaffi, na sadaukar da shi gare ku, ma su karanta.  Na gode da kun yarda da wanan shelan sakon Yesu Kristi da ku!*

*Ban taba na samu umarni da yau da kulun a kan litaffin mai sarki ko kuma ba wai na bayyane da kyau a kan lamurran tauhidi ba. Ama dai ni mai bin Yesu Kristi ne, kuma na kaunace litaffin mai sarki. Bari ni in raba wasu tunani da ku…*

**<u>Gabatarwa</u>:**

**In ana yin tambaya – 'waye ne Yesu'?' – ana wuri mai dadi!**

Watakila akwai jin haushi da Ubangiji, ko ba ka yarda da shi ba. ko watakila kana bin Ubangiji kuma kana ji Kamar baya nan. watakila kai musulmi, ko Hindu, ko Buddhist, ko wani addini daban ne. watakila kuma kana wuri daban ne, da ko kaima ba za ka iya ayyana ba… ba tare da la'kari ba, ko na yanda kana ji ba, Ubangiji na litafi–da ga rubutun farko zuwa na karshe – ya karbai ku, ya ma roka saboda ku yi tambayan: **'Waye ne Yesu?'**

Watakila kana da tambayoyi dayawa a kan wanan Magana, wato, a wanan takarda na zo in gwada amsa wanan tambayoyi, sai kuma in raba wadansu ilimi a kan shi. Abin guri na ban gaskiya shine litafi da ruhun mai sarki.

Na yarda da litafi akan – da duka rubutu na takardun da ya kai sittin da shida–wai ya zo daga Ubangiji ne. kaman ko wani abu mai kyau ko mai gaskiya, za a iya samun rashin fahimta da rubutun litafi, ko rashin amfani, ko kuma akwai shakka. Duk da haka, da duka kuskurin mutum a amfani da wanan litaffi, wanan litaffi, shi ne wurin zuwa ma mutum da yana so ya san ya da ake bin Ubangiji. Mutane da suka rubuta litafin mai sarki ba wai suka je makaranta ne ba, saboda kowa ya iya ya karanta. Ubangiji bai rufe kan shi ba a chikin litaffi, ya bamu inda zamu iya mu nime shi ne.
Yanzu zan raba da ku tunani na a kan wanan tambayan wai: **'waye ne Yesu?'**

## ***Waye ne Yesu?***

Litaffi ya koya muna cewa Yesu Kristi – yana nufi "Ubangiji mai ceto"– shi ne Ubangiji a jiki mai Kama da na mutum. Ubangiji ya sauko kasa daga aljanna, ya zama mutum, domin mu san shi da kyau sai kuma mu hadu mu zama daya da shi.

Yesu shi ne Ubangiji da ya zo a jikin mutum. ya zo ya gafarta da zunubin mu, sai ya bamu rai madawwami. Wanan shi ne Yesu, da kuma dalilin zuwan sa.

***Wahayi:***

Rubutun litafi ya ce muna wai wanan shi ne maganar gaskiya, da kuma mai wuyan fahimta.
Baza mu iya mu gane wanan gaskiyan ba, wai Ubangiji ya bar aljanna ya zo ya same mu a kasa, wanan ilimi ya yi kato ya fi mu, litafi ya gaya muna wanan gaskiya – gaskiya mai dadi– mai kato fiye da zukatan mu.
An ce muna wai wanan gaskiyan Ubangiji– Yesu kristi– shi ne ruhu da gaskiya' kuma zai zo muna ba da fahimta na hankali ba, ama ta wahayi na lamiri, har zuchiyan mu.

In kai – Kaman ni, da mutane da yawa– mu na kokari mu samu Ubangiji, ko inda mun sa shi ya dace a hankalin mu, na da wuya mu yarda ma lamirin mu da kuma zuchiyan mu su dauki iko. Ama da sanin ka, aboki na, duka abubuwoyin mahimanci a rayuwan ka– *abokanaye, iyali, murna, kauna, zaman lafiya, gafara, rahama-* wanan abubuwa su ba gaskiya gare da hankalin mu ba, ama na zuchiya da lamiri. Kusan ko wani lokachi, mun sa hankalin mu, da gafartawan mu, su lalatar da 'gaskiya na zuchiya' ko kuma zumunchi. ***ka taba ka bar kwakwalwan ka ya zo da farko kafin zuchiyan ka, sai ka yi nadama?*** !
In wato Ubangiji zai zama a chikin karamin kwakwalwan mutum wato shi karamin Ubangiji ne chikaikai.

An gaya muna daga litafin mai sarki wai, *'Ubangiji shi ruhu ne, kuma masu biyayya ya kamata su bi shi a cikin ruhu da gaskiya. '*Yesu da kansa ya ce akan kalmomin shi da wahayyi, *'kalmomi na ruhu da rayuwa ne.'*

***Ka taba ka ji kamar gaskiyan Yesu na da wuyan ganewa a kwakwalwa ama na da saukin konkwosawan kofan zuchiya?***

***<u>Sako'n Yesu Kristi:</u>***

Na da ban sha'awar kan da Yesu ya ba da kara domin mutane su bi Ubangiji. Bai zo da kudi ko da wadata ba. ba wai ya zo ya amsa tambayoyin tiyoloji ba. ya yi tambayoyi Kamar 'akwai mai kishin ruwa*? Ya zo wuri na ya sha … kowa da ya yarda da ni, da magudanan ruwan rayuwa zai kwarara achikin su. '*Yesu ya tambaya wa ne mai 'kishi', kuma ya yi alkawarin ruwan rayuwa. 'wanan maganganu bai dace da alladan zaman rayuwan mu ba; bai dace da hankalin mu ba ma. Ama dai ya soka da zurfi a chikin rai na mu.

***Wanan tambayan na Yesu– 'kana kishi?' – ya sake maimantawa a rai na mu?***

ko, na misali, Yesu ya tambaye jama'a, *'akwai mai gagaya?'* kuma ya ba da alkawarin hutu.

Yesu ya yi abubuwan mamaki, ama akwai manufa ma duka abubuwar mamaki da yayi. akwai lokachi da Yesu ya fada ma taruwan jama'a wai dalilin da ya yi duka abubuwan da ya yi saboda mu san wai zai iya cece mu ne. bai yi abubuwar da ya yi domin ya sa rayuwan wadansu ya yi soki ma lokachi kadan ba, ama domin a gan wai yana da gafara ma zunubin kowa, kuma ya rubuta sukaayen mu a aljanna.

***Me ne sako'n shi? Yane zan samu wanan 'rai', 'wanan hutu', wanan 'ruwan rai' a rai na?***

A nan ne sakon Yesu ya fafarta – a zahiri, kuma da kana…

Yesu ya ce, *'ni ne kofa, kuma duk wan da ya bi ni zai samu ceto.'*Yesu bai yi koyesuwa a kan Ubangiji ba; Yesu ya kira mu zuwa wurin shi soboda mu san Ubangiji, mafi zurfin abin da kake da shi a rayuwan ka a yanzu shi ne 'wani mutum', ba wani abu ko wani ra'ayi ba. ka yi tunanin shi ma minti daya. ***mene ya fi daraja a rayuwan ka yanzu haka?***
Na tabatar ma ka. Ubangiji baya cenzawa. Gaskiyan Ubangiji mafi darajan shi ne-kan shi. Nufin zuwan shi a kamanin mutum, shine domin kai da ni mu iya mu gani, mu taba da mu san shi. Saboda haka, dayan sukaan Yesu shi ne 'EMMANUEL', da ya nufi, *'Ubangiji yana tare da mu.'* Yesu –Ubangiji a kamanin mutum– ya zo domin ya siya da mu, yanzu da kowani lokachi.

***Ka na so ka san Ubangiji?***

***Imani:***

Yesu ya ce muna mu yarda da shi. abin da ya ce Kenan lokachin da ya na tare da jama'a, kuma sukaa ganin shi. *in suka iya sukaa ganin shi, me ya sa akwai nacewa akan yardawa da shi?* Abubuwa guda biyu suka shiga tunani na akan wanan maganan Imani

1. ***Abokin gaskiya zai yarda da kai!***

   Ka taba ka samu aboki da baka yarda da shi ba? Wanan mutum yana ganin ka kuma yana gaishe ka a duka wurin da kake; wanan mutum yana cikin zumunchi da kai, ama basu yarda da kai ba, Kaman suka rufe gefen zuchiyan su daga wurin ka. ***ka taba ka samu irin wanan zumunchi?***

   Yesu ya zo– Ubangiji a jikin mutum– ya zama tare da mu. sunan sa, Emmanuel, ya nufi, *'Ubangiji na tare da mu. '*[1]Yesu ba ya son mu gan shi kawai ba; ya zo domin mu yarda da shi kuma domin ya shiga zumunchi da mu. <u>*yardawa da juna shi ne abin da yana tabarta da zumunchi.*</u>

   Yesu ya ce, *'ni na kira ku, abokanaya na.'* Yesu kuma ya ce wai ba hanya da ke nuna kauna da ya wuce na bayar da rai'n ka

2. ***Na gani ba da yardawa ba!***

   Jama'a da yawa suka gan karfin shi, ama ba su yarda da shi ba. Watakila kai, Kaman ni, wadan su lokachi kana ce, *"in zan iya ganin Yesu da idanu na…"* gaskiyan shi ne, da yawan mu da suka gan shi da idanun su suma basu yarda da shi ba. Kusan ko wani lokachi da Yesu, ya yi abin mamaki, mutane suka juye ma shi baya. a karshe, mutane da suka 'gan' shi- wanda suka ji shi, wanda suka bi shi, ko wanda suka yi tafiya da shi, suka more abubuwan mamaki da ya yi- suka yi masa makarkashiya, kuma suka watsi da shi. an kashe shi da sa'afe a idanun wanan mutani.

   Saboda haka ne Yesu ya kira mu wurin imani, mu bi shi, ba wai na 'ganin' shi. lokachin da mutum ya gan shi, ya kashe shi. mutum ba zai iya ya bi abin da yake gani da idanun sa ko wani rana da duka zuchiyan sa ba. za mu iya bi na lokaci kadan, Kaman manzane'n sa ba ama a wani lokaci idanun mu, zuciyar mu, da hankalin mu za su kai ga fadiwar mu kuma ba za mu kai ga nasara ba. Za mu ma iya juya baya akan abubuwan da muke gani kuma mun soyanta.

   Yesu ya gaya ma Toma, manzon sa, '*albarka ga wada suka yarda ama ba da gani ba*.'

   Nan a duniya, Yesu yana so mu 'gani' da idanun zuciyar mu, kuma mu yi Imani – i.e. mu karba, bi, mu yi biyayya, da bauta. Yesu yana son zumunci na gaskiya da kowa, abota!
   Wata rana za mu wuce zuwa aljanna, inda idanun mu za su yi sapta kuma zuciyar mu za su tsayayya, kuma za mu gan shi fuska da fuska. Ama na

[1] Ishaya 7:14/Matiyu 1:23

yanzu, kiran shi ne Imani ne.

***Ka gan Kaman kana ‘ganin’ Yesu da idanun zuciyan ka***?.

**<u>Dukiya:</u>**

***Me ya sa Yesu ya na da wuyan 'gani' da kuma yin Imani? Me ya sa duka duniya ba su ji Yesu kuma su yi Imani ba?***

A lokacin da na karanta litaffi, na yi mamaki yada Ubangiji ya na ayukan sa, Daga farin lokaci. Ko da shi ke Ubangiji ya kaunace kowa daidai, wasu sun 'san' Ubangiji, kuma wasu ba su san shi ba. Wanan shi ne- kuma zai ci gaba – ba zai yiwu mu fahinta ba, mu gane, da kuma mu bayyana.

Haka ne yake lokacin da Yesu ya taka a duniya, ya yi wa'azi kuma ya yi abubuwan al'ajabi. Wadansu suka fadi a tafin kafafuwan shi sai suka ce '*kai ne Ubangiji!' wasu suka yi ma sa kallon raini, izjili da kuma kalubale ikon sa*. Ya zai zama haka? Ya wani mutum zai kale Yesu ya gan Ubangiji, sai wani mutun zai kale Yesu sai kuma ya gan talakawan mutum? Ba zan iya bayanna ba!
Ama abin da na gani a duka rayuwa da koyesuwan Yesu, shi ne wai ya nuna kan shi a hanya mai zurfi da tawali.
Ga zurfi da kuma tawali! A lokacin da mutum ya 'gan' Yesu a ainihin shi – Ubangiji tare da mu'- wato wahayi ya kai zuciyan mutum din, ya canza shi har abada abadin. *Ama saboda wanan wahayi na da zurfi da tsabta da shuru, yana iya wuce mu da wuyan gani. Ga hankalin mu na nan a karkawa saboda hayaniya da sha'awa a farfagayan rayuwa, har abubuwan Ubangiji ma su zurfi su na ta wuce mu*.

Yesu ya fada wani guntun misali saboda ya kwatanta gaskiyan nan. Ya ce 'mulkin sama Kaman dukiyan da an binne a fili. In mutum ya samu, sai ya binne kuma, sai kuma a cikin murnan shi ya sayar da komin da na da shi saboda ya saya filin.

***Kana ji kaman Yesu dukiyan da kuna farawan gani, ama mutane a kewaye basu gani ba?***

***Jini:***

Labarin Yesu abin mamaki ne! an gaya mana Ubangiji ya zo ya cece mu daga zunubai'n mu, da 'tabon' mu. Ka sani, zunubin mu mafi girma yana saba da barin sawun jinni. Jinni, tushin rayuwar kowa, na zubi in da akwai fada, da zaji, da rashin sa'a, da wurin da akwai mutuwa. Dukan mu muna da shi a hanun mu, kai tsaya ko a fakaice. Mu na zama a duniya da an gina a kan bawa da zaji, kuma dukan mu mun taba zubar da jinni ko kuma cinye kayan sata da ya farashi jinin mutani. Wanan gaskiya mai danye da kuma maradadi ne – ama zubi da jini ya na tsakiyan duhu na duniya da kuma rabuwan mu da ga Ubangiji

Saboda haka Yesu ya zo, ya na so ya cece mu daga zunubi da kuma duhu. Ya na so ya cece mu daga duka shan wuya, da abubuwan da mun yi da ba daidai ba. Ya na so ya warkar da ko wani rai, da zuciya, da kasan da mu na zama. An gaya mana wai Yesu ya bude hanyar '*fansa*' da '*gafara*' a hanya mai ba da mamaki da ruhaniya: ***Yesu ya dauke zunubi na mu zuwa jikin shi, sai kuma ya mutu da shi***. Wani aya a litaffi ya sa shi haka: 'Ya zama zunubi saboda mu'[2]

Yesu ya dauke laifi da kunya namu, ya mutu da shi. Ya bi ya tashi, ama zunubi na mu bai dawo da shi ba. Ya bar zunubai na mu a kabari, domin Magana haka, Yesu ya tafi da zunubi na mu sai ya da wo da gafara da sabon rayuwa mana.

Wani aya mai iko ya sa shi haka: jinin Yesu 'ya na fada maganganu ma su kyau' fiye da jinni na zunubin mu

Saboda da haka, in mun karbe Yesu da gafara na shi, mu na da godiya saboda jinin sadakar shi, ma 'jinin Yesu'.

***Ka na so ka zama a wankye a jinin Yesu?***

---

[2] 2 kwarintiyawa 5:21

**Ruhu:**

Yesu na da rai! Ya na da jiki kuma ya na aljanna. Wata rana za mu gan shi ‘fuska da fuska’.

Ama lokacin da Yesu yana gaya ma manzane wai ya yi kusan barin duniya ya tafi aljanna, ya gaya ma su cewa su samu farin ciki da tafiyan shi – kara su yi kuka- saboda  Ruhun ma sarki zai zo wurin su ya zama a cikin *su.*[3]

Ka gani, lokacin da Yesu na duniya, ya zo a kamani na mutum kawai. In da Yesu na wani kauye, wato baya wani Kenan. In dai yana sa hanun zaman lafiya a kan wani, wato bai sa a kan wani daban kuma kenan. Ya zo a kamanin mutum, saboda haka, na da iyakanci a sorari da lokaci Kaman mu

Lokaci da Yesu ya hau zu wa aljanna, ruhun Yesu, Ruhun mai sarki ya zubi a kan kowa a duniya. Saboda Yesu da zaman lafiyan Yesu zai iya zama a ko wani kauye, da kuma ko wani zuciya a lokaci daya. Saboda haka Yesu zai iya zama a zuciyar mu ba tafiya a gefen mu kawai ba.

Yanzu da Yesu ya gamar da aikin shi a duniya-mutuwa da tashiwa kuma, saboda ya bamu gafarci da rai madawwami-yana zama a aljanna. zamu hadu da shi a ruhun mai sarki.

In mun yarda da Yesu, zai zo ya same mu ta ruhun mai sarki, sai kuma ya zama a cikin zuciyan mu, rai’n mu da kuma ruhun mu- ‘Ubangiji na tare da mu

***Ka na so ka yarda da Yesu, kuma ka samu ruhun mai sarki a zuciya da rayuwan ka?***

---

[3] Yahaya 14:17,26,28

***Gayyata;***

Yesu ya ce; ni ne kofa, kuma ko wan da ya wuce ta kofan nan, zai samu.*'* (Yahaya 10:9)

***Ka na so ka gayyatar da Yesu cikin zuciya da rai na ka yanzu?***

Wannan shawara ce ta ruhaniya, acikin bayarwa da rayuwan mu ma Yesu zamu samu gafarci, da rai madawammi. a lokacin da ka sadu da Yesu, kana sabon hanya, kuma 'wan da na Kaman hasken zafin rana.*'* (Karin Magana 4:18)

Gan inda za ka iya salake gada daga rashin rai zuwa sani'n Yesu.akwai abubuwa guda biyu da zasu yi taimako da kyau in 'an yi'. na yi rubutun su a kasan nan, kuma sai na rubuta addu'a da za ka iya karanta da kuma addu'a na ka daga zuciyan ka:

1. ***Tuba na zunubi:***

   Dole a tuba daga zunubi. wanan mai wuya ne, ama wanda Yesu ne ya ce ka yi. Ya kamata ka zaba yanzu, wai da ikon Yesu za ka juye daga duka zunubin rayuwar ka – su kudi, sha'wa, kwadayi, rashin gaskiya, jaraba, zina, batsa, da soran su.

   Tuban zunubi 'daga zuchiya ne', kuma da wucen lokachi ya kamata a fara ganin Yesu a abubuwar ka da na gidan ka. watakila akwai abubuwa da ya kamata ka daina, sadarwa, yanke, yar da, da za ka rabu da su… inka fara bin Yesu, kuma ka bar hanyan zunubi (wato 'tuba'), wato ka fuskanta bin Yesu.

2. ***Imani a cikin Yesu kristi:***

   Mun yi maganan daraja da gakiya na Imani a kowani zumunci mai gaskiya. Yesu yana kiran mu mu yarda da shi. Yesu yana kiran mu mu yi wanan takan Imani kuma mu fadau a saman muryan mu wai muna da Imani a cikin sunan Yesu. na rubuta addu'a a nan da zai iya zama naka. dole addu'an ya taso da ga zuciyar ka
   Har inka tuba da ga zunubai'n ka kuma ka karba Yesu, a lokacin, zai sa ruhun mai sarki a cikin zuciyar ka, gafarta zunubai'n ka, kuma ya rubuta sunan ka a aljanna.

   **<u>Addu'a:</u>**

   ***Ya Yesu, na gode da ka kaunace ni.na gode domin ka mutu mani, na gode domin ka gafartar da zunubai na kuma ka bani rai madawammi.***

   ***Yau na tuba da ga zunubai na, kuma na sa Imani da yardawa na a cikin hanun ka.na rauka ka gafarce zunubi na, kuma ka zuba mun ruhun mai sarki.***

   ***Na gode, Ubangiji, domin ka gafartar da ni. na gode, Yesu kristi, domin ka cece ni. ka taimake ni yanzu in rike imani, kuma in bika da duka kwanan rayuwa na, sai ranan da mun hadu da kai fuska da fuska. a cikin sunan Yesu na yi addu'a, Amin!***

***Sabon rai:***

Idan har ka dauke matakin Imani a cikin Yesu, an cece ka! An gafarce ka! Ka zama ‘sabon mutum’. Wanan shi ne gaskiyan Ubangiji. Shi ne sabon sako na Yesu.

A matsayin sabon haifaffe mai bi, na da daraja ka fara karanta littafin mai sarki ko wani rana, da wasu mintoti a cikin addu’a da Yesu. Na da daraja kuma idan ka shiga ikilisiyar kirista mai kyau, saboda ka yi girma a cikin Imani da kuma goyon bayan soran masu bi.

Idan ba ka da litaffin mai sarki, ina bayar da shawara ka nema na aro ko saya wani gobai. Ka nema a kan layi ko kuma a shagon litaffi.

Abin da nake yi shi ne karatun surah daya a cikin ko wani rana. Wata kila ka fara a sakon **Luka**, sai kawai ka ci gaba.

A Nema ikilisiya mai kyau da daraja. A yi addu’a da kuma a tambayi Yesu ya kai ka a wanan shawara. A nema shawarar ikilisiya daga krista mai bi wan da ka sani kuma ka yarda da. A tabbata ana jen ikilisiya ko son daya a cikin sati, wan nan sadaukarwar Ubangiji ne. za ka iya canza wadansu abubbuwa a jadawalin ka, da kuma a cikin kudade, saboda wan nan ya faru. Ubangiji zai girmama ka saboda wanan!

Zan so in ji daga gare ku! Har in ka yi mataki a imanin nan, a bi ta gidan yanar jizo a shafi mai zuwa, tura ma ni sako ka sanar da ni. Zan yi murna da ku, da addu’a ma ku!

Albarka, dan’uwa na da yar’uwa na! har sai mun hadu da juna -a haddu’ar dangi! - Ubangiji ya albarkace, karewa, da kuma wadatar da ku a cikin sunar Yesu!

Domin Karin albarkatu, ziyarci gidan yanar jizona a kasa:

www.1peter1three.weebly.com

***‘Ubangiji ya sa muku albarka, ya kiyaye ku. Ubangiji ya sa fuskar sa ta haskaka, ya yi muku alheri. Ubangiji ya dubai ku da idon rahama, ya ba ku salama.’*** Litaffin Kidaya 6:24-26

*Nassosi da aka ambata:*

***Ubangiji na kiran mu mu bi shi***: 2 korintiyawa 5:20

***Sanin Yesu Kristi kadai, litafin shi, da ruhun shi***: 1 korintiyawa 2:2-3

***Ihami da kuskure na litafi:*** ibraniyawa 4:12/Irmiya 29:13 (see also Matiyu 4:1-11 & 2 Korintiyawa 4:2)

***Marubuta jahilai:*** Ayyyukan manzanni 4:13

***Nufin 'Yesu', 'Ubangiji mai kiyaye':*** Matiyu 1:21

***Yesu a jikin mutum:*** Ishaya 7:14/Matiyu 1:23; Ishaya 9:6; Yahaya 1:1-5,9,14; Yahaya 8:58/Fitowa 3:14; yahaya 10:30; yahaya 14:9; yahaya 9:38/Matiyu 14:33/Fitowa 20:5; Yahaya 5:46; Kolosiyawa 1:15-20; Ibraniyawa 1:3; Filibiyawa 2:6-11; Zakariya14:9/Ayyukan manzanni 4:12; Wahayi 1:13-18

***Yesu yana so ya gafarta kuma ya ba da rai:*** Luka 5:24; Yahaya 11:25-26; Yahaya 4:13-14

***Wahayin, ba zai yiwu a gane ba!***: Yahaya 6:37, 65; Matiyu 16:16-18; Romawa 11:33-36; Ishaya 55:8-9; Zabura 36:9; 2 korintiyawa 4:6; Yahaya 4:24 & Yahaya 6:63
***Imani a cikin Yesu:*** Yahaya 7:37-38; Yahaya 11:25-26; Yahaya 9:35; Matiyu 11:28-30; Luka 5:24; Luka 10:20; Yahaya 10:9; Yahaya 5:39-40; Yahaya 15:13-15

***Gani ba yardawa ba:*** Yahaya 11:45,53; Matiyu 26:56; Markus 15:25 (9 in the morning) Yahaya 20:29; 2 korintiyawa 4:6; 2 korintiyawa 5:7; 1 Yahaya 3:2; 1 korintiyawa 13:12

***Ubangiji yana son kowa daidai! :*** 2 Bitrus 3:9; 1 Timoti 2:4; Matiyu 18:14; Yahaya 3:16

***Bautan Kristi da kin amincewan Kristi:*** Yahaya 9:38; Matiyu 14:33; Yahaya 10:20; 2 Korintiyawa 5:16

***Wahayyi mai Zurfi da shiru:*** Matiyu 16:20; Markus 1:24,34,44; Markus 4:11; Ishaya 6:9; 2 Korintiyawa 5:16; Zabura 42:7; Matiyu 13:44

***Jini da yanci a cikin Kristi:*** Ishaya 1:18; Zabura 25:15; 2 Korintiyawa 5:17; Galatiyawa 2:20; Luka 4:18/Ishaya 61:1; Ishaya 42:3; 2 Tahiri 7:14; 2 Korintiyawa 5:21; Ibraniyawa 9:22; Ibraniyawa 12:24
Ruhu: Yahaya 14:1-4; Wahayin 1:13-18; 1 Korintiyawa 13:12; Yahaya 14:17,26,28

***Gayatta da sabon rai:*** Afisawa1:13-14; kolosiyawa 1:27; Karin Magana 4:18; Yahaya 5:24; Markus 1:15; Matiyu 3:8; Ayukkan manzanni 3:19; Romawa 10:9; Luka 10:20; 2 Korintiyawa 5:17; Ibraniyawa 10:25; Zabura 1; Joshuwa 1:9; Ibraniyawa 4:12/2 Timoti 3:16